# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kowa dabam Allah ya yi shi: Mutunta haƙƙin tsirarru
## Kashi na huɗu: Rayuwar ’yan luwaɗi a Cape Town

Wadda ta rubuta: Kerstin Poppendieck
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

Mai ba da labari

Ryan: ɗan shekara 22

Junior: ɗan shekara 23

Leonie: ’yar shekara 25

**Mai gabatarwa:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin kashi na huɗu na shirinmu na “Ji Ka Karu” mai suna “Kowa Dabam Allah Ya Yi Shi – Mutunta Haƙƙin Tsirarru”. A cikin shirin namu na yau za mu gana ne da waɗansu matasa guda biyu daga ƙasar Afirka ta Kudu waɗanda ake kira da suna Ryan da Junior. Waɗannan matasa sun haɗa ɗabi’u da dama iri ɗaya: dukkaninsu dai suna zaune ne a garin Cape Town, kuma shekarunsu sun zo ɗaya, sannan dukkansu masu neman maza ne ko kuma ’yan luwaɗi. Sai dai kuma duk da haka rayuwarsu ta sha bambam. Shi dai Ryan farar fatar Afirka ne, shi kuma Junior baƙar fata ne ɗan asalin ƙasar Congo wanda ya yi ƙaura zuwa Afirka ta Kudu. Ita dai wannan ƙasa ta shahara a matsayin ƙasar Afirka da take rungumar ’yan luwaɗi hannu bibbiyu. Shin wannan abu haka yake ko ba haka yake ba? Sai ku kasance da mu domin jin yadda abin yake. Yanzu sai ku biyo mu don mu ziyarci kowane ɗaya daga cikin matasan a garin Cape Town.

**Bayanin Ryan:**

*“Sannunku da zuwa. Sunana Ryan, me kuke so a kawo muku? Ga tsarin abincin da muke da shi. Amma dai da shawara zan ba ku, da kun yi odar hambaga. Ku yi mini haƙuri kaɗan, ina zuwa yanzu.”*

**Mai ba da labari:**

Ryan dai yana aiki ne a wani gidan abinci da ke Cape Town inda ’yan luwaɗi ke zuwa. Ko’ina ka duba sai launin ruwan hoda kake gani, masu kai abinci su ma suna sanye da singileti mai ruwan hoda, an liƙa furanni masu launin ruwan hoda a jikin bango. Wannan irin kaya ba kasafai aka saba ganinsu a jikin sabis ba. Sai dai kuma wannan gidan abinci mai suna ‘Beefcakes’ shi kansa na dabam ne. Domin duk ma’aikatan da ke cikinsa kaɗai ko ’yan luwaɗi ko ’yan maɗigo. ’Yan luwaɗi dai na nufin maza masu neman maza, su kuma ’yan maɗigo na nufin mata masu neman mata. Shi ma dai Ryan ɗan luwaɗi ne.

**Bayanin Ryan:**

*“Ina jin daɗin zamana a nan garin. Na yi sa’a da ya zamo mutanen wannan*

*gari ba ’yan sa-ido ba ne. Babu wata gaba tsakanin wani da wani. Kana iya zama duk abin da ka ga dama, babu wanda zai damu da kai sai dai ɗan abin da ba a rasa ba, amma dai na san zan iya sa gajeren wandona ruwan hoda ba tare da kowa ya damu da ni ba.”*

**Mai ba da labari:**
To fa a saboda wannan dalili ne Junior ya so zuwa garin Cape Town.

**Bayanin Junior**
*„Sunana Junior kuma shekaruna 23. Ni na fito ne daga garin Kinshasa na Jamhuriyar Dimukuraɗiyyar Congo.”*

**Mai ba da labari:**
Ga dai Junior nan a zaune a cikin ofishin wata ƙungiya mai suna “Passop”. Yakan yi aiki sa-kai ne a wasu lokutan. Ita dai ƙungiyar Passop ƙungiya ce da take taimaka wa ’yan gudun hijira ’yan luwaɗi ko kuma ’yan maɗigo domin su samu shiga ƙasar Afirka ta Kudu. Shi dai wannan matashi, wato Junior, ya fito ne daga Jamhuriyar Dimukuraɗiyyar Congo. Yau shekara guda ke nan yana zaune a wannan gari na Cape Town.

**Bayanin Junior:**
*“Na zo ƙasar Afirka ta Kudu ne saboda ina son na rayu a matsayin mutum mai ’yanci. Sam babu wannan damar a ƙasar Congo. A can ina rayuwa ne a cikin fargaba. Na shiga jami’a, amma na kasa yin karatu saboda ana nuna mini bambanci a kullum. Kasar Congo ƙasa ce ta masu ra’ayin riƙau. Mutanen garinmu da kuma ’yan gidanmu duk suna ƙyamatar irin rayuwar da nake yi. Don haka na nemi zuwa ƙasar da zan samu ’yanci kuma na ji daɗi. Ba ni da halin da zan iya zuwa Turai ko Amurka saboda haka sai na lalubo wata ƙasa a Afirka. Tun da an ce ƙasar Afirka ta Kudu ba ta ƙyamar ’yan luwaɗi sai kawai na zo nan.”*

**Mai ba da labari:**
Junior dai na daga cikin dubban ’yan gudun hijira daga ƙasashen Afirka

waɗanda sukan zo ƙasar Afirka ta Kudu saboda kasancewar sha'awarsu ta fi karkata ga irin jinsinsu. Gwamnatin Afirka ta Kudu ita ce take ba su mafaka. Wannan kuma ya sa ƙasar ta Afirka ta Kudu ta fita dabam daga sauran ƙasashen da ke nahiyar Afirka. Alƙaluman ƙididdiga da ƙungiyar Passop ta fitar sun nuna cewa a ƙasashe 38 daga cikin 54 na nahiyar ta Afirka, haramun ne mutum ya zamo ɗan luwaɗi. An sha nuna wa Junior bambanci a ƙasarsa ta Congo. Abin ma ya fi ƙazanta a lokacin da yake karatu a garin Kinshasa.

**Bayanin Junior:**

*"Na fuskanci matsalar rayuwa. Ko da yaushe ni kaɗai nake harkokina. Akwai 'yan luwaɗi masu yawa a jami'ar da nake karatu, amma kuma ba ma haɗuwa a wuri guda saboda akwai haɗari a cikin yin hakan. Don haka muke ɓoye wa kowa cewa mu 'yan luwaɗi ne. Ni karatun lauya nake yi, kuma su kansu malaman namu kan ci mini fuska su ce idan mutum ɗan luwaɗi ne ya saɓa wa ƙa'idar halitta, kuma su ba sa ƙaunar ganin ɗan luwaɗi a wannan jami'ar. Ba ma su kaɗai ba, har babata ma sai da ta yi ƙoƙarin hallaka ni. Don haka na ce wa kaina, bari na kama hanya, don kuwa ban ga ta zama ba a nan."*

**Mai ba da labari:**

Ga Junior nan dai yana tattaki a cikin garin Cape Town. Yana sanye da matsattsen *jeans* da kuma baƙar jaket, sannan kuma ya sa ja-gira da janbaki. Wannan fa abu ne da ba zai taɓa yiwuwa ba a ƙasar Congo. Shi kuwa garin Cape Town ana ɗaukarsa a matsayin garin da ya fi maraba da 'yan luwaɗi fiye da ko'ina a Afirka. Ana yi wa wannan gari ma laƙabi da 'gari mai ruwan hoda'. Sai dai kuma a wajen Junior, garin na Cape Town yana da wata siffa ta dabam.

**Bayanin Junior:**

*"Garin Cape Town yana marhabin da 'yan luwaɗi, amma fa idan kana zaune a lafiyyayen wuri. Yawancin 'yan luwaɗin da ke samun walwala duk fafaren fata ne. Kuma fararen fata 'yan ƙasar Afirka ta Kudu ne kawai suke fitowa fili su ilmantar da kansu da kansu game da harkar luwaɗi. Su kuwa sauran mutanen da suke cikin gari sun ƙi tsayawa su fahimci yanda abin yake. Gaskiya*

*wannan shi yake sa mu a cikin wahala.”*

**Mai ba da labari:**

Abin takaici shi ne ba wai zama ɗan luwaɗi ne matsalar ba a ƙasar Afirka ta Kudu, maganar ta launin fatar jikin mutum ce. Su fararen fata ’yan luwaɗi na rayuwarsu a fili cikin ’yanci a wannan gari na Cape Town. Amma idan kai baƙar fata ne abin ba haka yake ba. Mafi muni ma shi ne yadda ake yi wa mata baƙaƙen fata ’yan maɗigo fyaɗe. Mutane sun camfa a garin cewa, yi wa mace ’yar maɗigo fyade zai mayar da ita ta daina ta dawo kamar sauran matan da ba ’yan maɗigo ba, wanda kuma yin hakan zai sa maza su dinga sha’awarta. Shi kuwa Ryan da yake farar fata ne har ya zuwa yanzu ɓacin ran da ya gamu da shi ƙalilan ne a wannan gidan abinci.

**Bayanin Ryan:**

*“Wasu lokutan mukan samu wasu marasa kunya da ke ganin cewa za su more idan suka yi mana shaƙiyanci. Sai dai kuma ba ko da yaushe hakan ke faruwa ba. Ko ba komai dai, mu muna zaune ne a nan kamar uwa ɗaya uba ɗaya. Idan wani ya yi wa wani mai sabis guda ɗaya shaƙiyanci nan da nan guda biyar za su fito su nuna masa kurensa.”*

**Mai ba da labari:**

Ita kuwa Leonie ba ta ga dalilin nuna wata ƙyama ba. Abin da duk matar da ba ’yar maɗigo ba takan yi shi ne, zama a bakin hanya tana kallon mutane. A tunanin Leonie abin sha’awa ne a ce mutane sun bambanta da juna ta halayyarsu, da yadda suke shiga, da kuma yadda suke magana. Yawancin abokan Leonie dai ’yan luwaɗi ne. Ita ta kasa fahimtar dalilin da ya sa mutum zai damu a kan ko kai ɗan luwaɗi ne ko kuma kai ɗan maɗigo ne.

**Bayanin Leonie:**

*“Gaskiya dai ni ban ga suna da wani bambanci da sauran abokaina da ba ’yan luwaɗi ba. Duk yawancin abubuwan da suke ba mu sha’awa iri ɗaya ne. Dalilin da ya sa nake zama da su shi ne ba wai don su ’yan luwaɗi ba ne. Ita abokantaka ai magana ce ta mutumin da ka amince da shi, kasancewar*

*mutum ɗan luwaɗi ko ba ɗan luwaɗi ba, wannan kuma wani abu ne daban. Ni abu muhimmi a wajena shi ne muna da ra'ayi iri ɗaya, kuma muna jin daɗin kasancewa tare da juna."*

**Mai ba da labari:**

Har yanzu dai Junior bai samu aiki ba, don haka ko da yaushe a cikin rashin kuɗi yake. Sai dai kuma bai karaya ba. Yana nan yana fafutukar ƙwato 'yancin 'yan luwaɗi da kuma 'yan maɗigo a ko'ina cikin duniya.

**Bayanin Junior:**

*"Ni ban taɓa ganin mutumin da ya taɓa faɗa cewa, "daga yau ka zama ɗan luwaɗi" ba. Babu wanda ya taɓa tilasta mini zama ɗan luwaɗi. Ni kawai na samu kaina ne a yadda nake. Kuma akwai 'yan Afirka masu yawa da suke kamar yadda nake ɗin nan. Akwai su da yawa a kowace ƙasa ta Afirka."*

**Mai ba da labari:**

Ryan ma mai aiki a gidan abinci na 'Beefcakes' yana fatan cewa wata rana za a wayi gari babu wata damuwa ko mutum ɗan luwaɗi ne ko ba shi ba ne.

**Bayanin Ryan:**

*"Abin takaicin shi ne, mutane sun cika nuna wariya. Zan so a ce yau ga 'yan luwaɗi suna zuwa ko'ina ba tare da an muzguna musu ba. Sai dai mu yi ta haƙuri har hakan ta faru, ni dai ina da kyakkawan zato a kan hakan."*

**Mai gabatarwa:**

Da wannan buri na samun al'umma mai haƙuri da juna da Junior da Ryan suke da shi a garin Cape Town shirinmu na "Ji Ka Karu" ya zo ƙarshe a yau.
Idan kuna muradin sake sauraron wannan shirin da ma wasu da suka gabata, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/Ibe. Sai ku rubuto ku faɗa mana. Za ku kuma iya tuntuɓarmu ta shafinmu na 'Facebook'.